Babu cuta ba cutarwa

Daga Abu Sa'id al-Khudri - Allah Ya yarda da shi - cewa Manzon Allah - tsira da amincin Allah su tabbata agare shi - ya ce: «Babu cuta ba cutarwa».

[Hasan ne] [Ibnu Majah da Darakutni da wasunsu Suka ruwaito shi a matsayin Musnad]

Annabi - tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi - yana bayyana cewa tunkuɗewa kai da wasu cuta yana wajaba gargwadon nau'o'inta da yadda ta bayyana, ba ya halatta ga wani ya cutar da kansa ko waninsa daidai wa daida. Kuma ba ya halatta gare shi ya rama cuta da cuta; domin cuta ba a tunkuɗeta da cuta saidai ta hanyar ƙisasi ba tare da wuce gona da iri ba.

http://sunnah.global/hadeeth/ha/show/66531